# Rajin kawo sauyi da Yin Canji

Mahalarta taro za su ƙara sani game da ra'ayin rajin kawo sauyi ta hanyar gano wata matsalar da ta shafi al'ummarsu da kuma magance canje-canje guda biyu da suke so su gani a gaba wanda ya danganci matsalar.

# Mene ne rajin kawo sauyi?

## Kashi na Ɗaya

### Sanar da Ɗalibanka

Akwai al’amura da yawa a cikin al’ummominmu da kuma abubuwan da ke kewaye da mu da muke gode ma. Watakila muna godiya ga abokanmu. Zai iya yiwuwa cewa muna jin daɗin yin wasa a cikin wata ƙungiyar wasanni. Watakila muna so mu samu damar sauraron wata sabuwar waƙa daga wurin mawaƙin da muke so.

Haka kuma, wasu lokutan akwai al’amura game da al’ummarmu da ba su yi mana daɗi ba. Watakila makarantarka ta fito da wata sabuwar dokar sanya sutura, da ke buƙatar kaya masu tsada waɗanda ba za mu iya saya ba. Watakila wani zaɓaɓɓen ɗan siyasa na yin ƙoƙarin ƙirƙirar wata doka wadda ba ta yin la’akari da buƙatunmu. Zai yiwu zaɓuɓɓukan sufuri wurin da muke zama ba a tsara shi domin ya kai mu wurin da muke buƙatar zuwa ba.

Bari mu ce ka lura tashar motar bas ɗin ta tilasta ma dukkanku domin ku ɗauki motoci bas guda uku da kuma doguwar tafiya wajen cimma babban kanti mafi kusa.

### Tambayi Ɗalibanka

Ta yaya za ka yi ƙoƙarin canza wannan?

Shin akwai wasu mutanen da za ka cimma waɗanda za su iya taimaka maka?

Watakila kana da abokai waɗanda suka fuskanci irin waɗannan matsalolin kamar kai. Ta yaya dukkanku za ka tsaya ma kanku?

## Kashi Na Biyu

### Sanar da Ɗalibanka

A irin waɗannan yanayoyin, a kai a kai muna jin cewa abubuwa za su gyaru idan muka iya canza abun da ke damun mu. Wannan sha’awar ta tsayawa a kan abun da ka yi imani da shi da kuma ƙirƙirar canji shi ake kira “rajin kawo sauyi”

### Tattaunawa a Aji

A kan allon majigi a gaban ɗakin, sake duba shafin yanar gizon da aka yi amfani da shi a wajen rajin kawo sauyi. Bayyana yanda fom ɗin rajin kawo sauyi ya wakilci mutane, matasa a kai a kai, waɗanda suka gano cewa wata matsalar da take shafar al’ummarsu sannan kuma suke so su yi wani abu domin ƙoƙarin canza ta. Misalai daga Kasar Amurka sun haɗa da Fight For $15 da kuma Women’s March. Misalan da ke da abubuwa da suka shafi duniya sun haɗa da Global Voices, Greenpeace, da

World Wildlife.

**Sanar da Ɗalibanka**

Yanzu za mu bayyana wata matsala guda ɗaya a cikin al’ummarka da ka damu da ita sannan kuma da wasu matakan da kai da al’ummar za ku iya ɗauka domin ku warware ta.

# Aiki

## Aiki

### Aiki

Raba mahalarta taron zuwa ƙungiyoyi na mutum 3. Ba kowace ƙungiya lokaci a sashin da ake ciki a halin yanzu, da kuma a ƙalla cikakkun kwanaki, don 1) binciko wata matsalar da take yin tasiri a cikin al'ummarsu, gano a ƙalla hanyoyi guda biyu da matsalar ke shafar al'ummarsu da kuma hanyoyi guda biyu da za a warware matsalar, da 2) samar da wani kwalin sanarwa da ke samar da bayanai a kan matsalar da aka gano da mafitar da za su gabatar ma babbar ƙungiyar a matsayin wani ɓangare na "wata tattaunawa."

### Sanar da Ɗalibanka

A cikin ƙungiyoyinka,

1. Yi bincike sannan ka gano wani ɓangare a cikin al'ummarka (a "al'ummar" za ta iya kasancewa makarantarku, unguwa, ko wata ƙungiyar cikin gida da kake ciki) da kake so ka canza. Za ka iya yin magana da abokanka, malamai, da/ko iyali game da abubuwan da suke so su canza ko kuma game da matsalolin da suke shafarsu.

2. Ƙirƙiri wani kwalin sanarwa: Za a maƙala kwalayen sanarwar da kowace ƙungiya ta ƙirƙira a bango kuma za mu yi "wata tattaunawa" tare a inda kowane rukuni zai tattauna matsalar da suka gano da kuma yanda za a magance ta.

Dole ne kowace ƙungiya ta gano a ƙalla hanyoyi guda biyu da matsalar ke shafar al'ummarsu da kuma hanyoyi guda biyu da za a magance ta.

Ka zama mai fasaha: ɗauki hotuna sannan ka manna su a kan kwalin sanarwar [abun da ya fi dacewa, ka tabbata mahalarta taron suna da damar samun na'urar yin ɗab'i] don bayyana matsalar da/ko hanyoyin warware matsalar, ko kuma yin amfani da zane-zane, da taswira domin yin magana a kan iya matsalar da/ko mafita.

Ya kamata kowane kwalen sanarwa ya "tsaya da ƙafafunsa" — a wani ƙaulin kuma, ya kamata kwalin sanarwar ya kasance yana ɗauke da isasshen bayani a kan shi saboda wani ya iya duba shi/karantawa shi kuma ya fahimci matsalar da mafita ba tare da wani ɗan ƙungiyar ya yi bayani ba.

### Aiki

Ka ba kowace ƙungiya isasshen lokaci don su fara bincike da kuma samar da kwalin sanarwarsu. Ka tabbata cewa za a iya samunka saboda tambayoyi da bayar da

taimako. Yayin da babbar ƙungiyar suka sake haɗewa, suka sanya mahalarta taron suka maƙala kwalin sanarwarsu a bango, ba babbar ƙungiyar mintuna 20 domin su zagaya kuma su duba kwalayen sanarwar sauran ƙungiyoyin, sannan ka bayar da kusan mintuna 30 don kowace ƙaramar ƙungiyar ta gabatar da nasu kwalin sanarwar ga babbar ƙungiyar.

Wannan kayan karantarwar da Matasa da Kafar Watsa Labarai suka samar a Cibiyar Samar da Intanet &amp ta Berkman Klein; Jama'a a Jami'ar Harvard a ƙarƙashin lasisin Creative Commons Attribution-ShareAlike 4.0 International. Za ka iya yin amfani da wannan, har da yin kwafi da kuma shirya samar da ayyuka, ko kuɗi ko kuma wanda ba na kuɗi ba, kamar yanda ka siffanta. Matasa da Kafar Watsa Labarai a matsayin tushen da suka samar da ayyukan na ainihi da kuma raba wasu ayyukan da za su zo a gaba a ƙarƙashin sharuɗɗa ɗaya. Waɗannan da wasu ƙarin kayayyakin karantarwar su ma akwai su a intanet a Dandalin Kayayyakin Karatu da Rubutun Zamani na Berkman Klein.